# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na bakwai: Me ke faruwa?

Wanda ya rubuta: Nkoji C. Muhoho
Wanda ya tace: Maja Braun
Wanda ya fassara: Kabir Isa Jikamshi

**’Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Sama’ila: | ɗan shekara 17 |
| Bilkisu: | ’yar shekara 40 |
| Mariya: | ’yar shekara 43 |
| Hadiza: | ’yar shekara 15 |
| Adamu: | ɗan shekara 36 |

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu", inda a yau kamar yadda aka saba za mu ci gaba da wasan kwaikwayon nan na kiwon lafiya inda muke mayar da hankali kan yadda za a nisanci kamuwa da cutar gudawa.

A wasan da ya gabata kun ji yadda Sama'ila da Hadiza waɗanda abokan juna ne suka ɗauki nauyin koya wa sauran takwaroransu 'yan makaranta ƙarin hanyoyin kula da lafiyarsu, musamman ma bayan Sama'ila ya yi fama da wannan cuta. Uncle Adamu, jami'in kiwon lafiya na yankin, ya tashi haikan domin ya taimaka musu.

**Fitowa ta 1: A gidan Bilkisu**

Sama'ila, Bilkisu, Hadiza, Mariya

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Mama, anya kuwa, ba mu sayo abinci fiye da kima ba? |
| **BILKISU** | Ɗana, ka manta yadda kake cin abinci da yawa? Wannan abincin zai ƙare cikin sati ɗaya, ko ma fiye da haka. |
| **HADIZA** | Kuma ni ma mamata tana son cin abincin, ga shi kuma, dukaninmu muna sha'awar cin abincin a nan. |
| **BILKISU** | Haka ne, Hadiza, babu wanda zai zauna da yunwa a gidana, kuma ku abokai ne, waɗanda muke ɗauka tamkar 'yan gida ɗaya. |
| **MARIYA** | Bilkisu, kuna ta maganar abinci, amma ni wata irin masifar ƙishiruwa nake ji. |
| **BILKISU** | Sama'ila, don Allah, kawo wa Anti Mariya ruwan sha. |
| **SAMAILA** | Gaskiya, muna da wata matsala. |
| **MARIYA** | Wace irin matsala? Babu ruwa ne? Muna da duk irin wannan abincin, amma a ce ba ruwa? |

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Ba a tafasa ruwan ba. |
| **MARIYA** | To. Ni dai ban taɓa tafasa ruwan shana ba a duk tsawon rayuwata, ga shi kuma har yanzu ina raye kuma ina da lafiya. |
| **SAMA'ILA** | Amma yanzu Anti, mun san abubuwa masu yawa. |
| **MARIYA** | Sai dai hakan bai kashe mini ƙishiruwa ba. Ɗan wannan kaɗai, ba ni ruwan! |
| **HADIZA** | Mama, ki tuna fa da yadda yara suke yin kashi da fitsari a gefen rafi, ana wanke tufafi, shanu suna tattaka kashi, sannan su bi ta cikin ruwan da suke sha. Suna gurɓata ruwan da ƙwayar cutar da ke haddasa gudawa. |
| **SAMA'ILA** | Kada kuma mu manta cewa, bayan na yi bayan-gida a cikin lambunki Anti, lokacin da nake fama da cutar gudawa, ruwan sama ya wanke dagwalon da na bari a lambun, ya tura shi cikin rafin. Mai yiwuwa kuma, wannan yana cikin wancan ruwan shan… hmm! |
| **MARIYA** | Dakata, ya isa haka! Ka tafasa ruwan, zan jira ka. Ba na son in kamu da cutar gudawa. |
| **BILKISU** | Yara, tun da kun san kome a kan wannan, don me ba za ku haɗa kayan abincin ba, sai ni da Mariya mu dafa shi? |
| **HADIZA** | Kai, wannan ya yi kyau! |
| **SAMA'ILA** | Har da ni ma, Hadiza. Bari mu wanke dukan kayan lambun. Za mu wanke su da tafasasshen ruwa. |
| **HADIZA** | Daga nan sai mu yi ƙoƙarin tsane ruwan. |
| **SAMA'ILA** | An gama, aiki da cikawa. |
| **HADIZA** | Bari mu yanka naman. |
| **MARIYA** | Kai, ku yi hankali da wuƙar nan fa! |

**SAMA'ILA** Muna kula, Anti. Wayyo Allah! Kudaje. Ina jin naman nan ne ya shigo da su nan. Mai yiwuwa suna ɗauke da ƙwayoyin cuta ko kuma guba.

**HADIZA** Za mu hanzarta yanka naman, sannan mu rufe shi ruf.

**BILKISU** A rufe nama? Saboda me? Bayan nan da wasu 'yan mintoci za a dafa shi.

**SAMA'ILA** Saboda cikin kyaftawa da bissimillah ƙudaje za su sauka a kan naman, su dasa muggan ƙwayaye, su kuma saki ƙwayar cuta a kai. Idan muka ci naman, za mu haɗa da waɗannan ƙwayoyin cutar.

**BILKISU** Idan haka ne, zan tabbatar da cewa na dafa abincin sosai, domin in kashe waɗannan ƙwayoyin cuta da kuma gubar.

**SAMA'ILA** To, bari mu yi duka biyun.

**Fitowa ta 2: A gidan Bilkisu**

Bilkisu, Mariya, Hadiza, Sama'ila

**MARIYA** Bilkisu, abincin nan ya yi daɗi sosai!

**BILKISU** E, ya yi daɗi, amma ai dukanmu ne muka dafa abincin. Yanzu kuma sai ka taimaka mini, mu gyara teburin da aka ci abincin, a kai kwanukan da aka ci abincin a ɗakin dafa abinci.

**MARIYA** Kai, na gaji liƙis. Tun safe nake ta kwaramniya.

**BILKISU** Ni ma na gaji ƙwarai.

**MARIYA** Har yanzu muna da kwanukan da za mu wanke. Kina yin irin wannan tunanin da nake yi kuwa?

**BILKISU** Sama'ila, Hadiza! Ku bar kwanukan a cikin kwatarniyar wanke-wanke. Kowa ya gaji. Za mu wanke su gobe.

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | A'a, Mama, za mu wanke su yanzu. Idan muka bar kwanukan nan a nan, ƙudaje za su zauna a cikinsu, kuma za mu iya fuskantar hatsarin kamuwa da cutar gudawa. |
| **HADIZA** | Mama, ni da Sama'ila za mu wanke su. |
| **MARIYA** | Me kuke jin zai faru idan dukan yara za su yi aiki tuƙuru domin nisantar kamuwa da cutar gudawa? Babu shakka, da duniya ta samu ƙarin wani ci gaban. |

**MAI BA DA LABARI**

Mariya ta yi gaskiya. Idan dukan yara suka san hanyoyin kiwon lafiya kuma suka yi aiki da su, za a samu raguwar kamuwa da cututtuka da kuma mace-mace. Kuma wannan duka wani aiki ne mai sauƙi wanda mutane za su riƙa maimaitawa a kai-a kai, kamar wanke hannuwa da kuma abinci kafin a dafa shi. Daga bisani ɗan'uwan mijin Bilkisu, wato Uncle Adamu ya zo gidan su Sama'ila. Har yanzu wannan iyali suna da wasu tambayoyin.

**Fitowa ta 3: A ƙofar gidan Bilkisu**

Sama'ila, Adamu, Bilkisu, Mariya, Hadiza

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Uncle Adamu, lokacin da likitoci suka gwada ni a asibiti, sun yi mini bayani game da ƙwayoyin cutar da ke zama cikin 'yan hanjin mutum. |
| **ADAMU** | Wannan gaskiya ne. A ɗakin gwaje-gwaje, suna nuna irin ƙwayar cuta da kuma guba da mutum yake ɗauke da su. |
| **BILKISU** | Ke nan, kowa zai iya samun waɗannan ƙwayoyin cuta? |
| **ADAMU** | Kwarai kuwa, Bilkisu, kowa zai iya samu! |
| **MARIYA** | Mutum zai iya samun ƙwayoyin cutar, bayan kuma ana kiyaye dabarun kula da lafiya kamar wanke hannuwa da tafasa ruwan sha? |

| | |
|---|---|
| **ADAMU** | Ko da kina yin aiki da hanyoyin kiwon lafiya ne. Ki tuna fa, kina sayo dafaffen abinci daga gidajen sai da abinci, mutane suna musabaha da hannu. Sannan kuma muna taɓa abubuwa a sauran wuraren jama'a, da dai sauransu. Ta waɗannan hanyoyi za ka iya zama cikin kasadar ɗaukar ƙwayoyin cuta, ko da kuwa kana kiyayewa a cikin gidanka. |
| **HADIZA** | Ya kamata a duba lafiyarmu. |
| **ADAMU** | Wannan shawara ce mai kyau, Hadiza. |
| **MARIYA** | Lafiyata ƙalau, ba na yin gudawa, don haka saboda me za a gwada ni? |
| **BILKISU** | Ina son a gwada ni. |
| **HADIZA** | Ni ma haka. Uncle Adamu, abokaina na makaranta, su ma za a gwada su? |
| **ADAMU** | Kwarai! Za mu shirya da malamarku game da batun yin gwajin. Ai kamata ya yi ma in sake kai ziyara makarantarku cikin hanzari. |
| **MARIYA** | Mene ne manufar yin hakan? Idan alal misali, irin waɗannan ƙwayoyin cutar ko tsutsar cikin da ke cikina ba sa sa ni rashin lafiya, saboda me za a matsa masu? |
| **ADAMU** | Kada ki wawata mana! Idan har kina da ɗaya daga cikinsu, sannu a hankali za su gawurta. Yanayin 'ya'yan hanji wuri ne mai daɗi da zai dace ga irin waɗannan ƙwayoyin cuta su haɓaka. Idan tafiya ta yi tafiya kuma, sai cutar gudawa ta kunno kai. |
| **MARIYA** | Kai, Adamu, ka tsorata ni sosai! Ni ma za a gwada ni. |
| **ADAMU** | Da kyau! Na yi farin ciki ƙwarai. Zan yi shirye-shiryen da suka wajaba. Daga nan dukanmu sai mu tafi asibiti domin a gwada mu. |

**MAI BA DA LABARI**

Babu wanda yake son zuwa asibiti. Yawanci idan mun ziyarci asibiti, ko dai muna rashin lafiya ko kuma mun je mu gaishe da maras lafiya. Amma a wannan karon labari ya sha bambam. A yau, Sama'ila da 'yan gidansu da kuma makwabtansu sun tafi asibiti ne ba don a ba su wani magani ba, sai don kawai a gwada su ko suna ɗauke da ƙwayoyin cutar da ke haddasa cutar gudawa. Rigakafi ya fi magani.

**Fitowa ta 4: A ɗakin gwaje-gwaje a asibiti**

Adamu, Mariya, Sama'ila, Hadiza, Bilkisu

| | |
|---|---|
| **ADAMU** | Yauwa! Kowa ya ɗauki waɗannan robobin. Za ku ba da bayan-gidanku ɗan kaɗan, za mu kuma ɗauki jininku. |
| **MARIYA** | Suna son na sanya shi a cikin waccan ƙaramar robar? Wannan ba abin kunya ba ne? |
| **SAMA'ILA** | Anti Mariya, ba abin kunya ba ne. Wannan wani abu ne kawai da ya wajaba mutum ya yi. |
| **HADIZA** | Kin dai razana ne kawai, Mama. Kamata ya yi ki yi alfahari cewa kin yi wannan abin. |
| **BILKISU** | Mariya, ƙawata, bari mu yi wani gwajin domin jaririyata Fati. Idan da ni da ke mun san wannan, da har yanzu Fati tana nan a raye. |
| **MARIYA** | Haka ne fa. To, bari mu yi saboda jinjira Fati. |
| **ADAMU** | Da kyau. Bari mu ci gaba da abin da muka sa a gaba. Ku kawo samfurin bayan-gidan naku. |
| **BILKISU** | Adamu, idan suka yi nazari, kuma suka gano waɗannan abubuwan marasa kyau, daga nan kuma, sai mene ne zai faru? |

| | |
|---|---|
| **ADAMU** | Idan suka gano ƙwayar cutar da ke sanya ki rashin lafiya, sai su ba ki maganin da zai kawad da ita. |
| **MARIYA** | Haka ne! Idan ka yi niyyar ba mu maganin, don me ba za ka ba mu shi yanzu ba? Ka ba mu kwali guda kawai domin duka jama'ar gida. Ka ga kawai sai mu tafi gida mu raba a tsakaninmu, ba tare da sai mun yi wannan abin kunyar ba. |
| **SAMA'ILA** | Anti Mariya, ba abin kunya ba ne. Kuma abin bai da sauƙi kamar yadda kike yin bayani. |
| **BILKISU** | Mutum ba zai yi amfani da maganin wani ba, ba tare da izinin likita ba. |
| **MARIYA** | Saboda me? Bayan muna cin abinci iri ɗaya. |
| **ADAMU** | Dakata, Mariya, ya isa! Bari na yi bayani. Wannan yana da matuƙar muhimmanci, don haka a saurara sosai. Kowane mutum yana samun magani kwatankwacin nau'in ƙwayar cuta ko gubar da ke cikin 'ya'yan hanjinsa. Aiki da magani yana da wani irin tsari dabam. |
| **HADIZA** | Tsari? Mene ne haka? |
| **ADAMU** | Ana nufin ya wajaba ka yi amfani da maganin kamar yadda likita ya umarce ka. Mutum ya sha daidai adadi, a lokacin da aka ce, kuma a ci gaba da yin amfani da maganin tsawon lokacin da aka umarci mutum, ko kuma har lokacin da maganin zai ƙare baki ɗaya. |
| **MARIYA** | Idan kuma ba na jin wani ciwo, don me ba zan daina yin amfani da maganin ba? Saboda me zan kammala... yaya ma kake kiran kalmar? Tsari ko ƙa'ida? |
| **HADIZA** | Idan ba ki kammala ba, ƙwayar cutar za ta farfaɗo, sannan ta fara sake yaɗuwa a duk 'ya'yan hanjinki. Daga nan kuma, sai ki kamu da cutar gudawa. |
| **ADAMU** | Hadiza, bayaninki ya yi daidai, haka ne. Dukanku kuna da wasu ayyuka a gabanku. Bari mu tunkare su. Sai an jima. |

**Fitowa ta 5: A gidan Mariya**

Hadiza, Sama'ila

| | |
|---|---|
| **HADIZA** | Sama'ila, ka yi sauri! Ba na son Mama ta gan mu muna shan miyar dage-dagenta. |
| **SAMA'ILA** | Hmmmm, wannan dage-dage ta yi daɗi! |
| **HADIZA** | Bari mu sha! |
| **SAMA'ILA** | Amma fa ta yi sanyi, Hadiza. Mai yiwuwa za mu ɗumama ta? |
| **HADIZA** | Idan muka ɗumama ta, Mama za ta ji ƙanshin daga wancan ɗakin, kuma za ta san cewa muna shanye mata miyarta! |
| **SAMA'ILA** | Wane ne zai fi muni? Ɓacin ran mahaifiyarki, ko kuma mutum ya kwashi ƙwayoyin cuta, waɗanda za su sa ya yi gudawa? |
| **HADIZA** | Af! Haka ne, ka yi daidai. Na manta, akwai yiwuwar cewa abinci mai sanyi yana ɗauke da ƙwayoyin cuta. |
| **SAMA'ILA** | Zan ɗumama miyar. |
| **HADIZA** | Mama za ta yi fushi, kuma ka san ta. |
| **SAMA'ILA** | Kina son sanin yadda mutum yakan ji idan yana fama da cutar gudawa? |
| **HADIZA** | Ko kusa! Idan haka ne, bari mu yi fatar hancin mamarmu zai karkata wani wurin, kada ta ji ƙanshin miyar. |

**MAI GABATARWA:**

A halin yanzu dai Sama'ila da Hadiza suna rungumar hanyoyin kiwon lafiya dabam-dabam a gida. Sun koyi muhimman hanyoyin yin rigakafin kamuwa da cutar gudawa. Sun kuma sami damar jan hankalin iyayensu, suna saurarensu tare da ba su haɗin kai. Ana iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraro a www.dw-world.de/lbe.